Maye ya xagaka ya kai Baban Huzaim?

Daga Hanzala Bn Hizyam cewa Kakansa Hanifa ya ce: da Hizyam ka tara mun 'ya'ya na, saboda ina son inyi Wasiyya. sai ya tara su, sai ya ce: farkon abun da zanyi wasiyya shi ne cewa wannan Marayan nawa da yake kan cinyata in na mutu yana da Raqumi xari, wacce Muke kiranta a Jahiliyya Farantawa, sai Hizyam ya ce: ya Babana, naji 'Ya'yanka suna cewa: zamu yarda da wannan ne a gaban Babanmu idan ya Mutu ba zamu yarda ba, ya ce: to ai tsakanina da ku akwai Manzon Allah SAW, sai hizyam ya ce: Mun yarda sai Hizyam ya xaga da shi da Hanifa da Hanzala tare da su da yaron, kuma Hizyam ne ya goya shi a bayan abun Hawansa, yayin da suka isa wajen Manzon Allah SAW sai suka yi masa Sallama sai manzon Allah SAW ya ce: Mai ya taso ka ya Aba Hizyam? sai ya ce: wannan kuma sai ya daki cinyar hizyam da Hannunsa, sai ya ce: lallai ni ina jin tsoron kada tsufa ya cimmun ko kuma Mutuwa, shi yasa nake son nayi Wasiyya, kuma ni nace: cewa lallai farkon abunda zanyi Wasiyya da shi shi ne wannan Marayan nawada yake kan cinyata a bashi Raquma Xari, kuma muna kiranta a jahiliyya Kyautatawa, Sai Manzon Allah SAW yayi fushi har muka ga fushin a fuskarsa kuma yana Yana zaune sai ya durqusa kan Guiwoyinsa, kuma ya ce: A'a A'a Sadaqa Biyar ne, in kuma ba haka goma, in kuma ba haka ba to ashirin, in kuma ba haka ba Ashirin da Biyar in kuma ba haka ba Talatin in kuma ba haka ba Talatin da biyar idan kuma tayi yawa to arba'in" ya ce: sai suka yi masa bankwana da shi tare da Marayan akwai wani sanda, kuma da shi yake dukan Raqumin, sai Manzon Allah SAW ya ce: "Wanna sandar Mrayan tayi girma" Hanzala ya ce: sai ya kusanto dani zuwa Manzon Allah SAW sai ya ce: lallai ni ina da Yaya Maza ma'abota Gemu, da kuma qasa da haka kuma wannan shi ne Mafi qanqancinsu, ka roqa masa Allah, sai ya shafi kansa, kuma ya ce: "Allah yayi maka Al-barka" ko "An roqa maka Al-barka" Thayyal ya ce: kuma haqiqa naga Hanzala, ana zuwa da Mutum wanda fuskarsa ta kumbura ko dabba da Nononta ya kumbura sai yayi tofi a hannunsa kuma ya ce: da Sunan Allah sai ya sanya Hannunsa akan sa, kuma ya ce: akan wurin tafin Manzon Allah SAW sai ya shafeshi akai, kuma Thayyal ya ce: sai Kumburin ya tafi

[Ingantacce ne] [Ahmad ne ya rawaito shi]

Hanzala Bn Hizyam bada labarin Kakansa Hanifa ya ce: da Hizyam ka tara mun 'ya'ya na, saboda ina son inyi Wasiyya. sai ya tara su, sai ya ce: farkon abun da zanyi wasiyya shi ne cewa wannan Marayan nawa da yake kan cinyata in na mutu yana da Raqumi xari, wacce Muke kiranta a Jahiliyya Farantawa, sai Hizyam ya ce: ya Babana, naji 'Ya'yanka suna cewa: zamu yarda da wannan ne a gaban Babanmu idan ya Mutu ba zamu yarda ba, ya ce: to ai tsakanina da ku akwai Manzon Allah SAW, sai hizyam ya ce: Mun yarda sai Hizyam ya xaga da shi da Hanifa da Hanzala tare da su da yaron, kuma Hizyam ne ya goya shi a bayan abun Hawansa, yayin da suka isa wajen Manzon Allah SAW sai suka yi masa Sallama sai manzon Allah SAW ya ce: Mai ya taso ka ya Aba Hizyam? sai ya ce: wannan kuma sai ya daki cinyar hizyam da Hannunsa, sai ya ce: lallai ni ina jin tsoron kada tsufa ya cimmun ko kuma

Mutuwa, shi yasa nake son nayi Wasiyya, kuma ni nace: cewa lallai farkon abunda zanyi Wasiyya da shi shi ne wannan Marayan nawada yake kan cinyata a bashi Raquma Xari, kuma muna kiranta a jahiliyya Kyautatawa, Sai Manzon Allah SAW yayi fushi har muka ga fushin a fuskarsa kuma yana Yana zaune sai ya durqusa kan Guiwoyinsa, kuma ya ce: A'a A'a Sadaqa Biyar ne, in kuma ba haka goma, in kuma ba haka ba to ashirin, in kuma ba haka ba Ashirin da Biyar in kuma ba haka ba Talatin in kuma ba haka ba Talatin da biyar idan kuma tayi yawa to arba'in" ya ce: sai suka yi masa bankwana da shi tare da Marayan akwai wani sanda, kuma da shi yake dukan Raqumin, sai Manzon Allah SAW ya ce: "Wanna sandar Mrayan tayi girma" Hanzala ya ce: sai ya kusanto dani zuwa Manzon Allah SAW sai ya ce: lallai ni ina da Yaya Maza ma'abota Gemu, da kuma qasa da haka kuma wannan shi ne Mafi qanqancinsu, ka roqa masa Allah, sai ya shafi kansa, kuma ya ce: "Allah yayi maka Al-barka" ko "An roqa maka Al-barka" Thayyal ya ce: kuma haqiqa naga Hanzala, ana zuwa da Mutum wanda fuskarsa ta kumbura ko dabba da Nononta ya kumbura sai yayi tofi a hannunsa kuma ya ce: da Sunan Allah sai ya sanya Hannunsa akan sa, kuma ya ce: akan wurin tafin Manzon Allah SAW sai ya shafeshi akai, kuma Thayyal ya ce: sai Kumburin ya tafi

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/10957